# WASAN KARYA HARSHE



*Spider and Mantis*

Compiled by Sajida Mohammed

TATSUNIYOYI DA WASANNI  Ibrahim Yaro Yahaya

Kai jan mutumin nan,

Ka ɗauki jar sandar can,

Ka kori jar akuyar can,

Mai cin jar dawar can,

Ta gaba da gonar Jatau

*Spider and Mantis*

'Salamu alaikum matar Duba-Rudu'

'Maraba da baƙon Duba-Rudu'

'Duba-Rudu yana gida?'

'Duba-Rudu ya je kasuwa'

'To ke matar Duba-Rudu ba ni aron madubin Duba-Rudu in duba'

'Haba! Ni ma matar Duba-Rudu ban ɗauki madubin Duba-Rudu na duba ba, sai kai baƙon Duba-Rudu zan bai wa madubin Duba-Rudu ka duba?'

Da kwaɗo da ƙato suka je yawon ƙoto

Ƙato ya yi ƙoto

Kwaɗo ya yi ƙoto

Ƙato ne zai ƙwace wa Kwaɗo ƙoto

Ko kuwa Kwaɗo ne zai ƙwace wa ƙato ƙoto?